## TAFIYA BANGASKIYA     Babi na 1 - 7

Za mu fara nazari wannan shekara da rayuwar Ibrahim. Allah ne ya kira shi ya fara sabuwar rayuwa sa’an nan ya tafi inda bai sani ba. Wađannan surori suna nuna }arfinsa da rashin }arfinsa, begensa da tsoronsa. Ta wurinsa Allah ya fara aiki na shirin kawo albarka ba don iyalin Ibrahim da danginsa ka]ai ba, amma don dukan mutane.

Ta wurin Ibrahim Allah ya alkawarta zai kafa wata al’umma ta musamman. Al’ummar Isra’ila ce ka]ai za su san Allah yana tsakaninsu, da farko a alfarwa sa’an nan a haikali.

## Babi na 1     Kira da Fa]uwa

Farawa 12:1-20

TAMBAYOYIN TATTAUNAWA  MINTI 30

**MANUFA:** Domin mu yi biyayya a lokacin da Allah ya kira mu don mu đauki sabon mataki na bautarsa.

Yaushe ne ka san Allah ya kira ka don ka sauya zuwa yin wani abu a rayu-warka?

Mai yiwuwa mu sami sakewa:

- a wurin aikinmu
- a dangantakarmu
- a inda muke yin hidima ga ikilisiya

Me ka yi?

Yayin da muke nazarin rayuwar Ibrahim zai yi kyau mu tuna cewa ba shi da sani mai yawa a kan Allah na gaskiya kuma ya yi zama ne a tsakanin mutane masu bautar alloli da yawa. Shi mai shakka ne mai tsoro ne kamar kowane mutum, amma biyayyar da ya yi wa Allah ya shafe shi da iyalinsa da wasu al’umma.

**Lura:** {arfafa membobi su karanta su ayoyin babi na Farawa a gida. A lokacin nazari ku karanta ayoyi na tambayoyi kađai.

### Karanta Farawa 12:1-9

**Allah ya shiry hanya:**

1. Da Allah ya kira Ibrahim ya shirya masa hanyar sabuwar rayuwa wa]anne abu hudu ya fa]a masa ya yi (aya 1)?
   Wa]anne alkawura hudu Allah ya ba wa Ibrahim (aya 2-3)?

2. Ibrahim ya amsa kiran Allah ya fita ta wurin bangaskiya tare da matarsa, danuwansa, Lutu da kayan gidansa (aya 4-5).
   Wane karin tabbaci ne Allah ya ba Ibrahim lokacin da ya isa Kan’ana (aya 7)?

### Karanta Farawa 12:10-20

**Matarka ko ranka:**

3. Me shirin Ibrahim ya nuna game da halinsa na yadda ya san Allah a lokacin da ya shiga hatsari (aya 10-13)?
   Ba da misali yadda muke yi a lokacin da muka ji tsoro.

## CI GABA DA TAMBAYOYI

4. Mene ne abin da Fir'auna da mutanensa suka yi da ya nuna game da halayen al'ummar Masar (aya 14-16)?

5. A kan wane dalili ne Fir'auna ya kalubalanci Ibrahim (aya 17-19)?

   Ta yaya Allah ya nuna kulawarsa ga Ibrahim ko da yake ya yi wauta (aya 19-20)?

## TAKAICIN KOYARWA MINTI 5

Ibrahim ya ji da]in zama a Haran tare da iyalinsa da mallakarsa.

Kira da Allah ya yi na ya "fita" ya bar iyalinsa da al'ummarsa yana bukata dogara da yin biyayya yayin da Allah zai shirya hanyar rayuwar Ibrahim. Allah ya nuna wa Ibrahim inda yana so ya bi. Bai nuna masa taswira ba amma ya yi masa alkawari a nan gaba wanda Ibrahim ya same shi da wuyar gaskatawa. Alkawuran al'umma an shirya su don Ibrahim da iyalinsa:
- su zama babbar al'umma
- su yi suna
- su zama albarka

Mai yiwuwa Ibrahim ya sami kalubula a tunani tun da Saraya, matarsa ba ta haifuwa. Me za a ce da alkawarin da ya shafi duniya wanda ta wurin Ibrahim "dukan mutanen duniya za su sami albarka"! Yin biyayya da Ibrahim ya yi ya }arfafa mutane ya yawa kuma ban da muhimmiyar hanyar da Allah ya shirya wanda ta kawo albarka ga al'umma.

Ibrahim yana da dalilin da ya kamata ya ji tsoro shiga }asar Masarawa. Da Fir'auna zai ]auki dukan abin da yana so, ga shi fadawansa fadawansa suna son farin jini don ta hanyar ba shi abin da yana so. Da ya ]auki mataki na bangaskiya kuma aka tuna masa alkawarin da Allah ya yi a Kan'ana, sai Ibrahim ya yi shirinsa na yaudara. Allah ya shiga al'amarin, ya tilasata wa Fir'auna ya yi biyayya da mulkin sama da }asa, ya sa Ibrahim a kan hanyarsa don ya ci gaba da tafiyarsa.

## AYYUKAN YI MINTI 20

Ku rabu cikin }ungiya 2 ko fiye don ku tattauna tare da yin addu'a.

1. Don me yana da wuya a yau, fiye da zamanin Ibrahim, iyalai su ]auki mataki bangaskiya?

   Ba da misalin iyalin da sun yarda Ubangiji ya jagorance su a tafiyarsu.

2. Mutane biyu su fa]i yadda sun shiga hatsari amma Allah ya cece su.

   Ta wace hanya wannan zai }arfafa mu don mu dogara ga Allah cewa rayukanmu na hannunsa?

Karanta **Farawa 13:1-18; 14:8-24** cikin mako. Me za ka koya bisa ga halin Ibrahim?

**Wa}a:** "Yesu, Yesu, ina so in bi ka..."

## ADDU'A

* Gode wa Allah saboda lura da kiyaye rayukan wa]anda suka dogara gare shi.
* Yi addu'a domin zama da marmarin jin Allah lokacin da ya kira ku don ku canja hanyar rayuwaku sa'an nan ku dogara gare shi ya jagorance ku.

**HADDACEWA:** Farawa 12:2-3